Ruwayoyin Annabi Muhammad da magadansa sha biyu sun karfafa batun cewa dole ne a samu experts da zasu shiryar da muminai kan hakkokin Mahalicci a kan su, kamar yadda Imamin Ahlul Bayt na karshe yace: *"Saboda haka, dangane da Fuqaha wanda suka kare rayukansu da addininsu, sannan suka ki bin sha'awowinsu da son ransu, sannan suka zamo masu biyayya ga umarnin Master, irin wadannan mutanen ya halatta sauran mutane su bisu cikin alamuran addini (yin Taqleedi) kuma shi wannnan matsayi (na kusanci da Allah) ana samun shi ne kawai a wasu malaman Shi'a - ba dukan su ba." (Wasail ash-Shia, Vol. 27, Page 131, Hadith 33401)*

Akwai misalai da dama a lokacin Annabi Muhammad da magadansa ma'asumai inda suka umurci sahabbansu su shiryar da mabiyansu a wurare masu nisa kuma sun koyar da su hanyar zakulo dokokin musulunci akan 'sababbin abubuwan' da za su bullo.

## Yanayin da ake bukata wani ya kai matsayin Mujtahid

Mun iya fahimta cewa zama kwararre a hukuncin Musulunci*(fiqh)* da sauran ilimomin Musulunci bai isa ya mai da mutum Mujtahidin da kowa zai iya bi ba. Bugu da kari kan zurfin ilimin Musulunci da dole wani ya zama gwani akai, dokan Musulunci ya ce Mujtahidi yakamata ya zama 'yantaccen mutum (haihuwan halal) wanda ya wuce shekarun balaga, mai hankali, Shi'a na Ithna - Asheri kuma ya zamana, *adil* – wani siffa da za a fassara shi a zaman 'just' amma ya kunshi halaye na kwarai da shari'a, kaman tsoron Allah da kiyayewa daga duk abun da Shari'ah yake hani da shi da kuma aikata dukkan wajiban shi.

## Yaya za a gane Mujtahid da za mu bi

Yaya mutum mumini zai gane Mujtahidin da zai bi? Akwai sanannun hanyoyi uku: 1) Samun ilimin cewa shi malamin addini ne; 2) Shaidan *adilai* guda biyu , mutane masana akan cewa wannan Mujtahidi ne; 3) Wani shahareren matsayi wanda babu wanda yake shakkun cewa shi Mujtahidi ne.
Bugu da kari, mafi yawan malaman wannan zamanin sun yi tafi akan cewa ya fi dacewa abi Mujtahidin da shi *al-A'laam* ne. In muka dubi abun gaba dayan shi wannan yana nufin *'mafi sani'*, amma a wannan bayanin yana nufin mai hukuncin da ya kware a zakulo hukuncin Shari'ah daga asalinsu. Ana iya gane *Mafi sani* a hanyoyi uku da ake gane Mujtahidi, amma wani lokaci ya kanyi wuya wa malaman Shi'a su iya bambance mahukuncin da ya fi ilimi. A dalilin haka, ana iya bin *taqleedin* Mujtahidi fiye da daya a lokaci guda (amma ba ga mutum daya ba), yadda yake a yanzu ana da malamai 15 irin wadan nan wanda muminai za su iya zaba su bi, amma irin wannan yawaitan baya kawo rashin jituwa na al'amuran shari'a a cikin al'umman Shi'a.



# Amfanin Ijtihad da Taqlid

*"In bayan fakuwar Qa'im dinku ba wanda ya saura daga cikin masananku wanda: ke gayyata zuwa gareshi(Imam); shiryar da wasu zuwa gareshi; kare addininsa da hujjojin Allah; ceci raunanan bayin Allah daga sharrin Iblees (Shaitan) da rundunan shi, da kuma makircin makiyan (na Ahlul Bayt), kuma mutum ko daya ba zai saura ba (a bayan kasa) face ya bar addinin Allah. Amma, wa'yannan Malamai sun dauka wa kansu aikin kare zukatan raunannun mabiya, yadda jagoran jirgin ruwa zai kula da rayuka da lafiyan wa'yanda suke cikin jirgin. Saboda haka, wa'yannan (malamai – the Ulama) sune mafi kyau a wajen Allah, mai Karamci kuma mai Girma."*

Biharul Anwar, vol. 2, pg. 6, sec. 8, trad. 12

Samu karin sanin sahihin musulunci irin na Ahl al-Bayt – ka ziyarci:
www.al-islam.org/faq/

A rayuwan Annabi Muhammad *(tsarki ya tabbata a gareshi da iyalinshi)*, shi ne kadai mai iko a duk al'amura na addini da siyasa da kuma abubuwan da suka shafi addini da al'umma ana mika su zuwa gareshi ko kuma wanda ya ba wa iko (daga umarnin Allah) akan masu imani. Bayan rasuwar shi, jerin magadan sa – Imamai 12 – ya fara. Na farko daga wadanda karara aka ba ragamamar iko shine Ali ibn Abi Talib *(tsarki ya tabbata a gareshi)* kuma na karshe cikin magadan shine Imami na 12, al-Hujjat ibnil Hasan al- Askari *( Allah ya gaggauta bayyanar shi).*

Shugabancin Imam na 12 ya sha banban da na Imamai 11 da suka gabace shi tunda a hikiman Allah, a na bukatan ya shiga cikin fakuwa guda biyu rababbu kuma masu banbanci. Karamin fakuwan shi ta dauki shekaru 60 da kadan a lokacinne aka daura *zababbun wakilai* hudu. Su ke da hakkin isar da tambayoyin al'amuran yau da kullum daga muminai zuwa ga Imam, suna karbar kudaden Musulunci (Khumusi, Zakka, da sauran su) da kuma raba su yadda Imam ya ga ya dace, da sauran ayyuka.

Bayan mutuwar wakili na hudu a shekara ta 328 AH, aka kulle kofofin *zababbun wakilci*. Amma, shiriya bai kare ba, a tsarin umurnin da Imam na 12 ya bayar, za su bi malamai *(Fuqaha)* wadanda: *"...ke kula da ruhin su, da kula da addinisu, da kuma bin umurnin shugabansu (Allah)..."* Saboda haka, *'wakilci na gaba daya'* ya rataya a kafadar *ababen kwaikwayo na asali* (Mara'ja Taqleed).

## Menene Taqleed?

*An samu Taqleed* daga kalman larabci *'qal-la-da/yuqal-li-du/taqleed'* wanda ke da ma'ana 'kwaikwayo' ko 'bi'. Ba yana nufin "biyayya ido rufe" ba a yadda wasu suka fassara shi – sabanin haka, a tsarin dokar Musulunci, yana nufin cewa in wani ba zai iya tsamo dokokin musulunci daga asalinsu ba, amma yana komawa ga aikata hukunce-hukuncen da malamin da zai iya amfani da shi ke isarwa.

Bai zama wajibi akan mu muyi amfani da Taqleed ba, amma a yadda malamai suka lura, **zabin mu na farko** shine na zama Mujtahidi – *wanda ya kai matsayin yin Ijtihaadi – daman iya tsakuro dokokin Musulunci a 'yance daga asalin su,* kuma wannan ya wajaba a kan dukan muminai, amma in mutun daya ya iya wannan aiki, sauran mutane dukan an dauke musu wannan nauyi.

Tunda kai wannan matsayi ba zai yiwu ga kowa ba – kuma da kasantuwar cewa in kowa ya bada rayuwan shi ga 'karatun Muslunci' za mu fada karancin 'yan kimiyya, likitoci, injiniyoyi, artists, designers, da sauran su... **zabi na biyu** da a ka bamu kuma shine na yin taka tsantsan *(Ihtiyaat)* a bin dokan Musulunci. In wani ya zabi ya yi amfani da wannan tsari, sai kuma akan wani abu na musamman, tilas sai ya bibiya hukunce hukuncen Musulunci da Mara'ja na lokacin shi su ka fitar kuma ya zabi matsaya *" mawanda yafi taka tsantsan"* .

Ya kamata a lura cewa Taqleed ya kunshi abun day a shafi Shari'ah ne kawai; ba za a samu Taqleed a lamuran imani *(Usulu'd-din)* ba. Ya kasance dole Musulmi ya rike imanin sa a fundamentals na addinin shi bayan ya samu yakini a gaskiyan su ta hanyan kula da nazari. A gaskiya Qur'ani ma ya kushe duk wanda suka bi wasu a al'amarin imani ido rufe.

Amma, in mutum na so aikin shi ya yi su kwarai kuma yana so su karbu, to ya zama dole ya yi su a inuwan zabi uku da aka ba da a sama – rashin isa matsayin *Mujtahid*, rashin aiki da *Ihityaat*, da kuma rashin yin *Taqlid* ma sanannen Marja' zai iya mai da dukan ayyukan mutum (irin sallah da azumi) **batattu**.

## Hujjan na Hankali kan Taqleed

Yadda a kowane fanni na rayuwar mu, muna zuwa ga masana don su warware mana matsaloli dan ba za mu iya zama masana a kowane fanni da kuma cikin sashe irin na injiniya, likitanci, optometry, gyaran mota, da sauran su… a kullum mu kan kai matsalolin mu zuwa ga wanda suka karanta kuma sun kware a wani fanni na rayuwa. Fassarori da hukunce-hukuncen addini suma basu bambanta da irin wannan ba, a saboda haka, hankali ya nuna cewa in ba mu kai matsayin fahimtan Shari'ah ba, dole mu tambayi wadanda su ka kai wannan matsayi.

## Hujja na cikin Littafi a kan Taqleed

Alkur'ani yayi nuni da 'bin wasu' (wajen shiriyan addini) a wajaje da dama. A sura ta 9 na Alkur'ani, aya ta 122 za mu karanta cewa: *"Kuma baya kasancewa ga muminai su fita zuwa yaki gaba daya(zuwa wajen yaki) – saboda haka, don me ne wata jama'a daga gare su ba ta fita domin su nemi ilimi ga fahimtar addini, kuma domin su yi gargadi ga mutanensu idan sun komo zuwa gare su (domin su san hukunce-hukuncen addini)."*

Wannan ayar tana nuna cewa dole wasu daga ciki su wuce gaba su samu zurfin ilimin addini bayan sun dawo daga neman ilimi sannan sauran mutane sun dawo daga wajen yaki, sai su koyar da muminai game da hakkokin da suka rataya akansu na addini.